# Surah 84: Al-Inshiqaq - سورة الإنشقاق

بسم الله الرحمن الرحيم

[84:0] Bismi ***ALLAH***, Alrahman, Alrahim.*

إِذَا ٱلسَّمَآءُ ٱنشَقَّتْ ﴿١﴾

[84:1] Idan sama ta kece a bude,

وَأَذِنَتْ لِرَبِّهَا وَحُقَّتْ ﴿٢﴾

[84:2] Za ta gabatad da kanta ga Ubangijinta, ta qareshe.

وَإِذَا ٱلْأَرْضُ مُدَّتْ ﴿٣﴾

[84:3] Kuma za yi wa qasa lebur.

وَأَلْقَتْ مَا فِيهَا وَتَخَلَّتْ ﴿٤﴾

[84:4] Za ta fitad da abin da ke cikinta, sa’ad da take kece wa.

وَأَذِنَتْ لِرَبِّهَا وَحُقَّتْ ﴿٥﴾

[84:5] Kuma ta gabatad da kanta ga Ubangijinta, ta qareshe.

يَٰٓأَيُّهَا ٱلْإِنسَٰنُ إِنَّكَ كَادِحٌ إِلَىٰ رَبِّكَ كَدْحًا فَمُلَٰقِيهِ ﴿٦﴾

[84:6] Ya ku mutum, Lalle ne ka sa kai kenan zuwa gamuwa da Ubangijinka.

فَأَمَّا مَنْ أُوتِىَ كِتَٰبَهُۥ بِيَمِينِهِۦ ﴿٧﴾

[84:7] To, amma wanda aka bai wa littafinsa da damansa,

فَسَوْفَ يُحَاسَبُ حِسَابًا يَسِيرًا ﴿٨﴾

[84:8] To, hisabinsa zai yi sauqi.

وَيَنقَلِبُ إِلَىٰٓ أَهۡلِهِۦ مَسۡرُورٗا ٩

[84:9] Zai koma zuwa ga iyalinsa yana mai murna.

وَأَمَّا مَنۡ أُوتِيَ كِتَٰبَهُۥ وَرَآءَ ظَهۡرِهِۦ ١٠

[84:10] Amma wanda aka bai wa littafinsa, daga wajen bayansa.

فَسَوۡفَ يَدۡعُواْ ثُبُورٗا ١١

[84:11] To, nadama ta same shi.

وَيَصۡلَىٰ سَعِيرًا ١٢

[84:12] Kuma ya qone cikin Sa'ir.

إِنَّهُۥ كَانَ فِيٓ أَهۡلِهِۦ مَسۡرُورًا ١٣

[84:13] Da ya kan yi girman kai a cikin mutanensa.

إِنَّهُۥ ظَنَّ أَن لَّن يَحُورَ ١٤

[84:14] Da bai yi zoton zai komo ya yi bayani ba.

بَلَىٰٓۚ إِنَّ رَبَّهُۥ كَانَ بِهِۦ بَصِيرٗا ١٥

[84:15] Na'am Lalle ne, Ubangijinsa Ya kasance Mai gani a kansa.

فَلَآ أُقۡسِمُ بِٱلشَّفَقِ ١٦

[84:16] To, Na rantse da shafaqi.

وَٱلَّيۡلِ وَمَا وَسَقَ ١٧

[84:17] Da dare sa’ad da ta malale.

وَٱلْقَمَرِ إِذَا ٱتَّسَقَ ١٨

[84:18] Da wata idan ta yi lokutan sufayanta.

لَتَرْكَبُنَّ طَبَقًا عَن طَبَقٍ ١٩

[84:19] Za ku yi hawan wani hali kashi kashi.

فَمَا لَهُمْ لَا يُؤْمِنُونَ ٢٠

[84:20] To, ma ya sa, ba su yin imani?

وَإِذَا قُرِئَ عَلَيْهِمُ ٱلْقُرْءَانُ لَا يَسْجُدُونَ ۩ ٢١

[84:21] Kuma idan an karanta Alqur'ani zuwa gare su, ba su yin sujadah?

بَلِ ٱلَّذِينَ كَفَرُوا۟ يُكَذِّبُونَ ٢٢

[84:22] Dalili shi ne, wadanda suka kafirta, sai qaryata (*Alqur'ani*) suke yi.

وَٱللَّهُ أَعْلَمُ بِمَا يُوعُونَ ٢٣

[84:23] ***ALLAH*** Shi ne Mafi sani ga abin a suke tunanin sadarinsu.

فَبَشِّرْهُم بِعَذَابٍ أَلِيمٍ ٢٤

[84:24] Saboda haka, ka yi masu bishara da azaba mai radadi.

إِلَّا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ وَعَمِلُوا۟ ٱلصَّٰلِحَٰتِ لَهُمْ أَجْرٌ غَيْرُ مَمْنُونٍۭ ٢٥

[84:25] Amma wadanda suka yi imani, suka aikata ayyukan qwarai, suna da wani sakamako wanda ba ya yankewa.